# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Irmiya, Mutumin Hawaye



Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Jonathan Hay
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.



An haife Irmiya a cikin iyali masu bin addini a mulkin kasar Yahuda. Babansa, Hilkiya, shi firist ne. Iyalinsa sun zauna a wani gari mai suna Anatot, ba da nesa ba daga Urushalima. Watakila iyayen Irmiya sun yi tunani cewa Irmiya shi ma zai zama firist. Amma Allah yana da nasa shirye-shirye.




Lokacin da aka haifi Irmiya, mutanen Allah ba sa rayuwa bisa ga Kalmar Allah. Kusa kowa da kowa, daga sarki zuwa ma'aikata na kasa-kasa, sun bauta wa allolin karya – har ma cikin Haikali mai tsarki na Allah.
3
Lokacin da Irmiya shi matashi ne, Allah ya yi magana da shi. "Na san ka tun kafin ma haife ka," Allah ya gaya wa Irmiya, "kuma ina da shiri za ka yi magana a madadina."
4
Kiran Allah ya so ya ba wa Irmiya tsoro. "Ah, Ubangiji Allah!" ya yi ihu. "Ban iya magana ba, gama ni yaro ne." Ya fi a ce da shi yaro ne – gama ya kai shakaru ashirin. Amma Irmiya bai yarda cewa zai iya yin magana a madadin Allah ba, game da muguntan da ke kewaye da shi.
5
"Kada ka ji tsoro," Allah ya tabbata masa. "Tafi duk inda na aike ka. Ka fada duk abin da na gaya maka ka fada.
Ina tare da kai kuma zan fanshe ka." Sa'an nan Allah ya yi wani abu na musamman. Allah ya taba bakin Irmiya.
6
Allah ya ba wa Irmiya karfi da karfin hali da hikima. Ya yi magana da karfin hali, yana tunashe wa mutane cewa Allah yana kaunarsu kuma yana so ya taimake su. Amma babu wanda ya saurare shi. Ko sarki ma.
7
Har ma firistoci suka yi fushi da shi suka ce masa ya bar yin magana game da Allah. Akwai kuma annabawan karyan da suka ce Irmiya ba ya fadin gaskiya.
8


Irmiya ya tunashe mutanen cewa, wajen shekaru darin da suka wuce, mulki na arewa na Isra'ila sun yashe Allah. Abokan gabansu, Assuriyawa, suka ci nasara a kansu sai suka kwashe Isra'ilawa zuwa wani kasa mai nesa.
9
Yanzu mutanen Yahuda, mulki na kudu, sun yashe Allah. Abokan gaba yanzu suna a hanyar zuwa! Ko Allah zai bari a ci nasara a kan mutanensa a kwashe su zuwa bauta su ma?
10
Mutanen dai sun amince da gumakansu. Ko gumaka za su cece su daga abokan gabansu? A'a! Allah ne kadai zai cece su. Mutane suka ji fushi da Irmiya, sai suka fara kullu-kullen kashi shi. Amma Allah ya tsare bawansa.
11
A karshe, Allah ya fada wani abu wanda Irmiya ya yi mamaki. Allah ya ce, "Kada ka yi wa wadannan mutane addu'a. Ba zan saurare su ba sa'ad da suka yi kuka gareni don neman taimako."
12
Irmiya ya ja wa sarki kunne cewa ba zai ci nasara a yakinsa da sojojin Babila ba. Sarki ya yi fushi ya jefar da Irmiya a kurkuku. Har a cikin kurkuku, Irmiya ya ci gaba da wa'azi da amince wa da Allah.
13
Bayan da fita daga kurkuku, Irmiya ya sake yi wa sarki da mutanen wa'azi don su tuba su koma ga Allah su kuma amince da Shi.
Wannan karo, sarko ya gangaro da Urushalima zuwa wani bakin duhu.
14

**Amma Allah yana aiki a zuciyar sarki. A boye sai ya fanshe Irmiya ya tambaye shi mene ne Allah yake so sarki ya yi. "Ka tafi hijira, kuma Allah ya ce za ka rayu," wannan shi ne amsar.**





**Sojojin Babila suka ci nasara a kan Urushalima da duka Yahuda. Suka saukar da bangon birnin da duka gine-ginensu, suka kokkone komai da komai. Allah ya ce mutanen za su tafi zaman bauta har shekaru saba'in, sa'an nan zai dawo da su zuwa Kasar Alkawarin.**





**Irmiya, Mutumin Hawaye**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Irmiya**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**



# KARSHE

28

60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**